NAFI ƘARFIN KISHIYA!
Gajeran labari.

NA
FATIMA SUNUSI RABI'U
Ummu Affan

*_Shafi na farko_*

“Wai Sakina akan me kike magana? Nifa sam ban fahimce ki ba?” Gyara zama wacce aka kira da Sakina tayi, kafin cike da tsegumi ta ce“Ki yarda da ni Wasila, maganar daga majiya me ƙarfi najita.”
Wata uwar ashar da ta saka tare da miƙewa tsaye cikin tashin hankali, yarda ƙirjinta kuwa ke bugawa da sauri-da-sauri, abin zai ba ka mamaki. Sakina ba ta an kara ba sai ji tayi an shaƙi wuyanta, ai tuni ta fara zare ido cike da kakari domin ba ta san lokacin da Wasila tazo kusa da ita ba sai shaƙarar ta ji. Nan fa ta fara zare ido cikin tsananin tsoro, a zuciyarta kuwa tuni ta fara danasanin sanar da ita wannan batu, sam ta manta da mugun tsananin kishin Wasila, wacce zata iya komi akan mijinta.
Cike da ƙaraji da masifa bakinta har kumfa ya ke, saboda masifar da ke cinta, har zuwa lokacin hannunta na wuyan Sakina ba ta saketa ba ta ce“Kin san abin da kike cewa? Mijin nawa kike faɗar kinji yana neman ƙara aure? Ko har kin manta da wacece ni kuma Bashir mijina ne ni ɗaya? Ko shi ya tabbatar da hakan mijina ne ni kaɗai, wallahi ina da rai Bashir shi da aure sai dai ko a lahira, amma da raina ina numfashi a doran duniya to ni ɗaya zan zauna a gidana.”
Cikin tsananin galabaita Sakina ta fara neman hanyar ƙwatar kanta ta hanyar yi mata magiya da kuma daɗin baki.
“Wasila kiyi haƙuri, ina tsammanin ba ke ce wacce ake faɗa mini ba, ai ke nasan kin fi ƙarfin kishiya, kishiya sai dai a gidan wasu.” Sakinta Wasila tayi ta faɗi jagab bisa kujera, har lokacin bakin Wasila bai dena kumfa ba. Cikin wani sauti ta ce“Wallahi ni Wasila na fi ƙarfin kishiya, daga ni ba ƙari daga yayana sai mijina a kuma gidana, duk wacce ta shirya tazo mu zuba shege ka fasa, nifa akan mijina zan iya koma menene.” Sakina da ke nishi sama-sama da sauri ta suri zakarta, takalmi a hannu ta bar gidan.
Tun bayan fitar Sakina ta ke zagaye a falonta, ko maƙiyarta bata so ayiwa kishiya balle ita, ai ita ko shiri ba ta yi da wacce tasan mijinta ya taɓa auren wata ma balle kuma me kishiya.
Yaranta biyu da suka dawo daga makaranta sai sallama suke, amma sam bata ji su ba, sai da ƙaramar ta ƙaraso kusa da ita tare da taɓata, firgigit ta kalleta. “Ummi mun da...” kallon da ta ga uwar ta watsa mata ne yasa ta kasa

ƙarasa maganarta.

Jiki a sanyaye ta zame hannunta tare da wucewa ciki, domin idan da sabo sun saba da irin yanayin mahaifiyar tasu da bai musu daɗi, duk da kasancewarsu ƙananun yara. Domin babban wato Na'im shekararshi goma sha biyu, ita kuma Ni'ima tana da shekaru goma dan tazarar shekara biyu ce tsakaninsu.

Na'im kuwa tun da ya ga yanayin mahaifiyar tasu daman, kitchen ya wuce domin saka abinci.

Wasila kuwa kasa haƙuri tayi sai da ta ɗauki wayarta ta kira lambar Bashir, har ta tsinke bai ɗauka ba, kira uku bai ɗauka ba aifa sai hankalinta ya tashi, zuciyarta ta fara mata saƙe-saƙe, yanzu haka yana gurin wata ne. Ji ta ke zuciyarta kamar zata faso ƙirjinta ta fito saboda tsabar zafin kishi, da sauri ta suri key ɗin motarta tayi ficewarta, ba tare da tayi tunanin yanayin da yaranta zasu kasance ba.

Tuƙi kawai ta ke, amma gaba ɗaya hankalinta baya jikinta, burinta kawai ta kai ga isa office ɗin shi domin tasan abin da ke faruwa, shin yana ma office ɗin? Ko ya tafi zance ne? Abin da zuciyarta ke hasaso mata kenan.

Wacce ta hango daidai kwanar kamfanin da Bashir ke aiki ya sa ta jan wani mugun burki, yayin da zuciyarta ke harbawa da ƙarfi.

Ko kashe motar ba tayi ba ta fito da sauri, har da gudu ta haɗa domin ta cimmata, gabanta tasha tare da cin ƙwalarta.

Zaro ido tayi tare da cewa “Kamar Anty Wasila na ke gani ko? Idan ban mance fuskarki ba.”

Huro hanci Wasila ta fara cike da ɗacin zuciya ta ce“Ke bari fa kiji ni ba a munafurci da ni, me kika biyoyi ta hanyar kamfanin da mijina ke aiki? Saboda an rasa miji shine ake bi ƙwararo-ƙwararo da lungu-lungu domin mazajen mutane su gani, to bari kiji ni nafi ƙarfin kishiya kuma mijina yafi ƙarfinku daga ke har Yayar ta ki, don ni ƙawa ta kai irin shekarun Yayarki Zinatu ba aure to na barta har abada, da bazan tsaya amin sagegeduwa ba, bar ganin kuna yayan Malam ko Malum-malum ne.”

Uwani kuwa (Wacce akaci ƙwala) kama baki tayi cike da mamakin jin abin da ake faɗa akan Wasilar ya tabbata, da tana ƙin yarda yanzu kuwa dole ta yarda, idan ban da ƙarfin halin Wasila daga ta ganta tabi hanyar kamfanin da mijinta ke aiki, wannan wanne jahilin kishi ne.

Cike da takaici ta ce“Yanzu saboda Allah kin min adalci kenan? Wucewa fa kawai zan yi hanya ce ta kawo ni, ni ban ma san mijinki na yana aiki a wannan kamfanin ba” “Hmmm! ashe ma ko?” Wasila tayiwa Uwani tambayar rainin wayau, tana wani girgiza tana karkaɗa jiki saboda tsabar jin masifa.

Sakin ƙwalar Uwani Wasila tayi ganin abin da ya gigita ƙwanyarta, jikinta har tsuma ya ke cike da tashin hankali ta ɗaura hannu aka tare da fasa wata uwar ƙara...

NAFI KARFIN KISHIYA!

Gajeran labari.

NA
FATIMA SUNUSI RABI'U
Ummu Affan

*_Shafi na biyu_*

Da gudu ta ƙarasa gurin, sam basu lura da ita ba sai ganinta suka yi. Tana zuwa bata yi wata-wata ba ta shaƙi wuyan budurwar, kallonta ya ke cike da mamakin irin haukanta, ganin tana niyyar kai yar mutane barzahu ya yi saurin shiga tsakiyarsu tare da zare hannayenta daga cikin wuyan budurwar.

Cikin hargowa ta ce“Wallahi ba zai yuwu ba, yau ko ni ko wannan munafukar” Kokarin ture shi ta ke ta ƙarasa in da take sakamakon bayanshi da ya mayar da ita. Ganin tana niyyar mishi hauka a titi dan mutane har sun fara taruwa ya ce“Ke wai lafiyarki?”

“Ai dole kuwa ka tambaye ni lafiya, tun ka tare da wannan shegiyar tana maka fari da ido da murmushi, yau ko ni ko ita a gurin nan” Wani tsalle tayi ta chakumi wuyan budurwar ta fara gara kanta da bangon katangar kamfanin.

Cikin zafin nama ya fincikota tare da sharara mata mari, cikin faɗa ya ce“Wasila ke wacce irin mahaukaciyar macece? Me ke damunki ne?” Wasila wacce ta hantsila gefe saboda marin da tasha jin abin da ya ce ta taso da sauri tana wani irin kuka ta sake chakumar budurwar tana faɗin “Wallahi bazan barta ba, akan ta Bashir ka mare ni? Yau ko ni ko yarinyar nan.” Sam ya kasa ƃanƃare Wasila daga jikin yarinyar saboda gaba ɗaya ta gama haukacewa ta zamo kamar wata me aljanu.

Mutanan da suka taru kuwa sai kallonsu suke, yayin da waɗanɗa suka fahimci faɗan suke tur da irin zuciyar Wasila. Wasu kuwa matsowa suka yi suna ba da haƙuri, amma Wasila tayi kunnen uwar shegu da mutane. Da ƙyar Bashir ya iya tura Wasila mota, sannan ya tura budurwar motarshi ya tadata suka bar gurin, ganin ya tashi motar ita ma gyara zama tayi ta kunna tata tare da bin bayanshi.

Asibiti ya yi niyyar kai Hafsat, amma ganin Wasila na bin shi yasa ya nufi gida da ita. Ganin Bashir ya yi hun a gate ɗin gidan iyayenshi yasa Wasila ƙara jin ɗacin rai, kenan yar uwarshi ce? Auren dangi zai yi? Wasu hawayen baƙin ciki suka zubo mata a fili ta furta “Daman Hajiya ta ce sai Bashir ya ƙara aure, wannan ce yarinyar da ta ke son haɗasu kenan? To wallahi indai ina numfashi auren nan anbar yin shi.”

Motarta ta kunna, tana tafe tana kuka zuciyarta kuwa jinta ta ke kamar wuta saboda zafin da ta ke mata.

Tana shiga yaran zaune a falo suna home work, da gudu Ni'ima ta tashi ta ruga jikinta “Ummi oyoy...” Lafiyayyen marin da ta zubawa yarinyar ne ya sa

ta kasa ƙarasa maganar da tayi niyya, zubewa tayi a gurin tare da fashewa da wani gigitaccen kuka.
Cikin faɗa ta ce“Iskancin banza, kin san abin da ke damuna za kizo kina min wani oyoyo, to oyoyon ya ci ubanshi sakaryar yarinya kawai.” Wucewa tayi sama ba tare da ta kula da halin da yarinyar ta ke ciki ba saboda tsananin kishin da ke cin ta. Ganin wucewarta da sauri Na'im ya ƙaraso gurin yar uwarsa tare da kamata, shima tuni ya fara hawaye yana share mata jinin da ke fita baƙinta wanda sakamakon marin da Wasila ta mata ya fashe ya ce“Ni'ima kiyi haƙuri, kin san halin Ummi ba san mu ta ke ba amma kike shige mata, Abbu ya fi ƙaunarmu idan ya dawo zai kai ki asibiti” Gyaɗa kai Ni'ima kawai tayi alamar to, amma har cikin zuciyarta ta ke jin son jin ɗumin mahaifiyarta. (Allah sarki ya mace kenan).
****
“Bashir! Wacce magana kake min haka mara daɗin ji?” Kasa ya kuma yi da kai cike da ladabi ya ce“Ayi haƙuri Hajiya, kuskure ne baza a ƙaraba” “Au! kuskure ko? to bari kaji sai na nunawa Wasila tabbas tayi kuskure tun da ta duki yarinyar nan, daga aikenta wajenka amso min saƙo zata jiwa yar mutane ciwo irin haka? Wallahi wannan karon sai nayi maganinta na gaji da abin da ta ke min, za tasan kuwa tayi kuskure, kai kuma sallamme da baka iya kataɓus akan mace sai kayi ta zuba ido tun da ta gama da kai, ni kuwa nafi ƙarfinta kuma wallahi sai ta gane kurenta.”
Shi dai Bashir idan ban da ayi haƙuri babu abin da ya ke cewa.
Girgiza kai kawai Hajiya ta ke, a zuciyarta tana jin tausayin ɗan nata saboda irin wannan fitinanniyar mata da ya yi gamo da ita me mugun baƙin kishi mafi muni da munana, gaskiya mata da yawa suna hauka a wajen mugun kishin da bai da amfani, abin takaicin ma wasu suna sane sun sani Allah ya halastawa namiji auren mace fiye da ɗaya, amma suke kishi na jahilan mata me yasa mata ba zasu yi kishi irin na matan Annabi (S A W) ba?
“Ka tashi ka bani guri, ni nasan hukuncin da zan ɗauka, tun da kai dai Wasila ta fi ƙarfinka, wallahi sai na nuna mata ba ta fi ƙarfin kishiya ba.”
Jiki a sanyeye ya mata godiya tare da fita, Hajiya ta bi shi da kallon takaici da tausayi.
Bashir yana tuƙi yana tunanin irin halin Wasila, wanda ko a mafarki bai taɓa tunanin hakan zata faru ba, tunanin farkon haɗuwarsu ya yi, yarda Wasila ta ke yarinya mai kunya, gashi ta sami tarbiyya daga iyayenta matunan ƙyirki.
Tushen labarin..

NAFI KARFIN KISHIYA!
Gajeran labari.

NA
FATIMA SUNUSI RABI'U
Ummu Affan

*_Shafi na uku_*

Tushen labarin:
Bashir ɗa ne ga Alhaji Safiyanu da Hajiya Maryam, dukansu mutanan arziki ne, Alhaji Safiyanu Allah ya hure mishi yana da rufin asiri, yaransa uku Bashir ne babba sai ƙannansa biyu Hamza da Batula. Sun yi ilmi sosai duka biyun boko da arabi sannan sun sami tarbiyya.
Malam Tajaddin sunan mahaifin Wasila, Malami ne sannan ɗan kasuwa, ƙaramin ɗan kasuwa ne yana da dai rufin asiri tun da ana samun na sawa a baka. Tsakanin gidajensu ba nisa duk a layi ɗaya suke, Wasila tana shugowa gidansu Bashir kasancewar Batula ƙawarta ce, tun da Bashir ya ga Wasila ya ji yana sonta ya sanar da mahaifiyarshi, sanin Wasilar tana da tarbiyya ta bashi izinin ya nemi yarjewarta, in da cikin lokaci ƙanƙani suka fara soyayya, tana kammala secondry aka musu aure.
Da farko suna zamansu lafiya, inda daga bisani Bashir ya lura Wasila tana da mugun kishi don ta dawo sam bata san ganin wata mace ta raɓeshi, ada yana sharewa a tunaninshi duk cikin son da ta ke mishi ne, bayan haihuwarta ta farko ne ya fara soyayya da wata yarinya domin ara'ayinshi baya son zama da mace ɗaya ya fi son biu koma fiye da hakan tun da yana da halin riƙe su, kuma yana da tabbas zai iya sauke nauyinsu, a wannan neman auren ya ga hauka, in da anan ta ke kowa ya gano mugun kishi irin na Wasila daga yan uwanshi har na ta, iyayenta sun mata faɗa amma a banza, ba dan yaso ba a lokacin dole ya haƙura da neman aure.

Bayan haihuwarta ta biyu ma, ya nemi wasu aure har sau uku, amma bala'in Wasila kesa ana fasawa dan wasu iyayen matar da kan su suke cewa sun fasa ba zasu kai yarsu ga halaka ba. Idan har yana san zama lafiya da Wasila to dole fa kar ya yi hirar wata a gabanta gashi ko yaransu ba ta kula da su, bata ba su wani lokacinta saboda zafin kishinta.

Numfashi Bashir ya sauke daidai hun ɗinshi a bakin gate ɗin gidanshi. Yana parking ya fito yana tafiya a hankali kamar kazar da ƙwai ya fashewa a ciki, ba dan komai ya ke wannan sanyin ba sai dan gudun abin da zai tarar gidan, tabbas fitinanniyar mata da ban ta ke kuma mace tagari ita ce sila ta zaman lafiya, kuma ƙwanciyar hankalin miji, idan kayi dace da mace ta gari tabbas ka dace da rabin farincikin gidan duniya.

Har lokacin yaran suna falo, suna ganin mahaifin nasu da gudu suka tarbeshi cikin farinciki, shima duƙawa ya yi daidai tsayinsu ya rungumesu cike da so da ƙaunar yaran na shi.
“Ni'ima me ya sami bakinki?” Ya tambayeta ganin yar gurin ya ɗan tasa kuma ga bushasshen jini. Turo bakinta tayi cike da yarinta sai dai ba ta ce komai ba, Na'im ne ya ce“Abbu, Ummi ce ta mareta” Numfashi ya sauke kana ya ce“Kunci abinci kuwa?” Yanzu ma Na'im ne ya ce“Da muka dawo

School mun ci, amma yanzu Ummi ba ta kuma girki ba.”

Hannunsu ya kama zuwa sama, bayan shigarsu zaunar da su bakin gado ya yi sannan ya ɗauko musu yogut da donut a furiji, sannan ya faɗa wanka, shiyarwa ya yi cikin doguwar jallabiya sannan ya kwashi yaran zuwa falo, da kanshi ya shiga kitchen ya dafa musu taliya fara da ya ke ya ga ragowar miya, fitowa ya yi daidai ana kiran magrib hakan ya sa ya kama hannunsu duka suka yi alwala sannan ya ce Ni'ima tayi sallah kan au dawo.

Sai da suka yi isha'i sannan suka dawo lokacin Ni'ima har ta fara gengaɗi, tana da ya yi suka fara cin abincin da dama ya aje a falo kan su dawo, suna gamawa kowa ya yi hamdala, rakasu ya yi har ɗaki tare da musu addu'a sai da ya ga sunyi barci sannan ya nufi ɗakin Wasila.

Ita kuwa, tun dawowarshi ta ganshi, kuma duk abin da ya faru tana hangensu ta window, zafin kishin da ta keji ne ya hanata fitowa, duk da yunwar da ta ke ji amma taƙi fitowa domin kar ma ya ga warginta ya rainata in dai akan kishiya ne.

Sallama ya yi, a ciki ta amsa tare da kauda fuska, ƙarasowa ya yi cike da barkwanci ya ce “Matata uwar yayana, sannan uwargida a gidan Bashir!!” Wata miƙewa tayi ƙirjinta har bugawa ya ke ta ce“Uwargida, me kake nufi da wannan kalmar?” cikin sanyin murna da gudun fitina ya ce“Uwargidana kuma amaryata, ai Bashir na Wasila ne” Wani sanyi taji a ranta amma duk da haka ba ta saki fuska ba ta kuma cewa“Bashir wacece na ganku tare dazun?” Girgiza kai ya yi tare da samun guri ya zauna bakin gadon ita ma ya jawo hannunta ya ce“Wasila ki rage wannan mugun kishin wallahi, Hafsat ce yar gidan Umma Salamatu Hajiyarmu ce ta aiketa amsar saƙon da na faɗa miki jiya na Umma Salamatu ne.” Numfashi ta sauke duk da hankalinta bai kwanta ba dan tasan akwai aure tsakaninshi da Hafsat tun da yar ƙawar Hajiya ce, ßata fuska tayi “Amma Bashir me yasa baka kaiwa Hajiya saƙon da kan ka ba? Kasan kuma ba na son ganin ko wacce mace ta raßar mi kai?” Saboda a zauna lafiya ya ce“Na sha'afa ne uwargidana.” Da sauri ta ce“Kuma amarya a gidan Bashir Abbun Na'im da Ni'ima” Duka suka yi murmushi da wannan chaftar suka kwanta barci...

NAFI KARFIN KISHIYA!
Gajeran labari.

NA
FATIMA SUNUSI RABI'U
Ummu Affan

*_Shafi na huɗu_*

Washe gari da farinciki suka tashi, hakan ya sa Wasila shiga kitchen in da ta haɗa musu breakfast. Sannan ta shiga bedroom ɗin yaran, zaune ta iske su suna karatu, kasancewar tun asuba Abbunsu ke tadasu suyi sallah, sun ri ga sun saba yin karatun tare da Abbunsu, duk ranar da bai shugo ba sai suka yi su biyun.

Murmushi ta saki, “Yan biyun Abbu da Ummi, kun tashi lafiya?” Duƙawa suka yi suna gaisheta, ta amsa cikin fara'a cike da jin daɗin tarbiyyar da Abbunsu ke ba su, domin shine ƙashin komai.

Wanka ta sa suyi ɗaya bayan ɗaya tana chuɗasu, sannan ta taya su shiri cikin uniform ɗinsu, tare suka fito parlourn.

Murmushi Bashir ya saki cike da farinciki, ji ya ke ina ma kullum suna kasancewa cikin farinciki kamar irin yau? Har suka iso bai sani ba, sai da Wasila tayi masa tafi a fuska ya ɗago furgigit “Tunanin me kake?” Ta tambaya cike da tuhuma.

“Tunaninki, mana.”

Ya faɗa cikin ƙayatarwa, wani ƙayataccen murmushi ta saki.

Haka suka karya cikin farinciki, bayan sun gama sallama suka mata, har mota ta rakasu.

Yaran ya fara kaiwa School sannan ya wuce gurin aiki.

Karfe takwas na dare!

Zaune suke a parlour cikin farinciki, gama dinner ɗinsu kenan.

Karar buɗe gate suka ji tare da shugowar motoci, duka a furgice suka miƙe, buɗar da Wasila ta jiyo ne tafi komai ɗaga mata hankali.

Kofar parlourn da ake bugawa ne yasa ta sauri dawowa a hayyacinta, kan ta ɗago har ta hangi Bashir yana buɗewa. Sakin baki da hanci Wasila tayi ganin Hajiyar su Bashir rungume da wata an rufe mata fuska da mayafi, sannan ga wasu mata su biyar da ke take musu baya.

Guri suka samu tare da zaunawa, Bashir sai sannu ya kewa Hajiyarshi tare da gaishe su. Wasila kam tana tsaye ko zama ta kasa, dubansu kawai ta ke.

Hajiya ta ce“Ko ki zauna, ko ki tsaya, ko ki gaishe ni, ko ki kalleni duk ɗaya, wannan dai Hafsat ce, ada ƙanwa ta ke a gurin Bashir yanzu kuma mata”

Ai wani uban ihuw! Wasila ta saki tare da kururuwa faɗi ta ke“Na shiga uku na lalace, wayyo Allah na rantse da Allah ban yarda ba, ƙarya ne sharri akewa Bashir bai aureta ba, wallahi idan ta kasance matarshi sai na kasheta!!” Nan ta fara watsi da duk abin da yazo hannunta.

Da sauri mutanan suka miƙe ganon tana watso musu abu, kar ta kassara su. Batula da ta shugo yanzu da sauri tayi kan ta tana ƙoƙarin riƙeta, dakatar da ita tayi ta hanyar ɗaga mata hannu.

“Dakata! Karki ƙaraso ai da ke aka haɗa kai aka nuna min iyakata, ita Hajiyar tana da kishiya ne da ta ke so dole ni sai anyi mini? Ko kuwa ke ke Batula tun da kika yi aure mijinki ya taɓa miki maganar kishiya ne balle ya auro? Ni kuka tsana ba kusan ganina ni ɗaya a gidana saboda baƙinciki, me yasa dangin miji ba ku da adalci ne? Ku ta ke laifinku kuna hango na

yayanku da na yayunku.”
Jikin Batula ya yi mugun sanyi, me yasa har yanzu Wasila ta kasa gano mijinta da Yayanta suna da banbanci ba, wajen halitta.
Da gudu Wasila tayi sama tana kuka me cin ruhi da gangar jiki.
Hajiya ko ajikinta ta ce“Zaman Hafsat raɗau a gidan nan ko anƙi ko an so.”
Bashir kuwa komai yazo mishi a bazata, haka suka kai Hafsat ɗakin Bashir.
Hajiya ta ce“Kai kuma sallamamme me tsoran mace, sai ka zuba ido sakarai kawai, a jiki gaka namiji har namiji amma a gida mace ke juya ka kamar waina.”
Bai iya cewa Hajiya komai ba, har taja zugarta suka fita, da sauri ya nufi ɗakin Wasila.
Abin mamaki bai ganta ɗakin ba, toilet ya leƙa ko tana kusa, nan ma bai ganta ba, “To ina ta shiga?” Ya tambayi kanshi bai da amsa, fitowar da zaiyi ya hangi wuta naci a ɗakin shi.
A mugun tsorace ya ƙarasa, ai jin ihu kamar muryar Hafsat ga ta yara yasaki kusan suman tsaye, ko da ƙafarshi ya kasa ɗagawa saboda tashin hankali, ga har lokacin yana jin ihuw, da sauri kuma ya yi baya wayarshi ya ɗauko ya ƙira yan kwana-kwana domin wutar yanzu ta fara yawa, jin maganar mutane a waje ya sashi saurin fita, gashi tare ne, damma da hasken wutar nepa, nan mutane suka fara ba da temakon gaggawa Bashir kuwa ba baka sai kunne saboda tashin hankali ma, bazaka taɓa iya gane halin da ya ke ciki ba, gashi nan kamar mutum-mutumi, ƙwaƙwalwarsa ta zamo kamar ba komi.
Daidai isowar yan kwana-kwana sai kuma ga Hajiya tare da police dan ko gida basu kai ma aka kirata cewa tazo ba lafiya gidan Bashir wuta ta kama.
“Wallahi idan ta kasance matarshi sai na kasheta.”
Maganar da Wasila tayi ta tuno hakan yasata fashewa da kuka taje ta taho da police.

Lokacin da suka iso an samu an kashe wutar, sai dai da ƙyar aka ƙwaƙwulo gawar Hafsat wacce ta ƙone sosai, haka Na'im da Ni'ima, domin da Batula zata fita ta ce su shiga su taya Auntynsu hira, don tasan da wuya Bashir ya kwana ɗakinta a yau, ita kam Wasila lokacin da mugun kishinta ke cinta idanuwanta sun rufe sam tana hawa saman kitchen ta wuce tare da ɗaukar jarkar gas da ashana ta nufi ɗakin sam bata kallon gabanta tana zuwa ƙofar ɗakin ta kwarara gas ɗin tare da cilla ashanar don idanuwanta sun rufe tayi alƙawarin Hafsat ta bar kwanan gidan....

Nikam na ce fans ina Wasila ne?

NAFI ƘARFIN KISHIYA!
Gajeran labari.

```LABARIN GASAR MATASAN MARUBUTA 2021```
```

```Group 5```

```Jigo: Akan Zazzafan Kishi.```

NA
FATIMA SUNUSI RABI'U
Ummu Affan

*_Shafi na biyar_*

Wasila ɗaga hannu tayi ta ɗaura a kai tare da kurma wani uban ihu! daidai shugowar Bashir wanda ya ƙarasa da sauri bakin gadon da ta ke zaune, duka hannayenta ya riƙe, cikin kuka ta ce“Bashir da na shugo ɗakin nan, kasan tunanin da na fara?” Girgiza kai ya fara da cewa“A a sai kin faɗa.”
“Wai nasakawa Hafsat wuta na ƙonata.” Zaro ido ya yi har bai san lokacin da ya saki hannunta. Ta ɗaura da cewa“Wai na ƙona mata ɗaki da ita a ciki har da yarana duka biyu, kuma duka sun mutu, kai kuma kana cikin wani hali, sannan ga Hajiya da Police sun ƙaraso ga maƙota da ke ta tofin Allah tsine a kaina.” Shuru Bashir ya yi, yayin da idanuwanshi ke kanta cike da al'ajabi, sai yanzu ya fahimci abin da Wasila ke magana akai, nufinta da ta shugo tunani ta faɗa akan hakan da kuma abin da zai faru idan hakan ta kasance. Cikin sanyin murya ya ce“Wasila ki sawa zuciyarki ruwan sanyi, ki rage mugun kishi, nasan duk a kaina kike wannan zazzafan kishin, shiyasa na ke tausaya miki, kiyi haƙuri mu rungumi ƙaddarar da ta doso mu a yanzu na ƙaruwa da muka samu ta Hafsat.”
Sosai hawaye ki zubar mata cikin zafin kishi ta ce“Na fasa aikata wancen da nayi niyya, domin nayi tunanin makomata da ta yarana, nasan daga ƙarshe ni zan faɗa a halaka kuma na barka a duniya daga ƙarshe wataƙil ma ka auro huɗu rana ɗaya.” Bin ta ya yi da kallo cike da mamaki duk a tunaninshi ta saduda ne ashe ma yanzu wasa farin girki. Fita ya ga tayi da sauri ya bita cike da tsoro dan gudun abin da zai je yazo, tabbas Wasila ta furgita shi kuma ta fara bashi tsoro. Kitchen ya ga ta shiga hankalinshi ya sake tashi “To ko gas ɗin zata ɗauko?” Ya tambayi kan shi, ganin ta fito salin-alin ya saki wata gwauran numfashi. Ɗakinta ta shiga ba tare da ta ce mai ci kanka ba, Parlour ya zauna domin ba zai iya shiga ko wanne ɗaki ba domin gudun irin abin da zai je yazo.

Wasila kuwa tun da ta shiga ɗaki ta ke kaiwa da komowa cike da tashin hankali, zuciyarta kamar zata faso ƙirjinta ta ke jinta, tabbas zai ta aikata abin da tayi niyya shine kawai mafitarta, domin idan ta kashe Hafsat aikin

banza tayi, domin zai iya auren wata daga baya, abin da zata aikata yanzu kuwa shine yafi mata daidai don wallahi gara kowa ya rasa.

Bawan Allah Bashir yana zaune parlour har ya fara hamma can kuwa ya fara gyengyaɗi, zuwa can kuma sai barci mai nauyi ya ɗauke shi har da mun shari. Wasila wacce baƙin kishinta ke cin ta kuwa ko run tsawa ta kasa, lokacin da ta tabbatar ya yi barci ta fito, domin tana yawan leƙenshi, cikin sanɗa ta fito parlourn tare da nufarshi gadan-gadan domin zuciyarta ta gama ƙeƙashewa akan abin da tayi niyyar aikatawa.

Tana zuwa in da ya ke ta runtse idanuwanta da ƙarfi, bayan ta zaro wuƙar da ta soke a ƙugu, tayi alƙawari sai dai duka su rasa shi domin sai ta cire mishi mazaƙuta kowa ya huta, (Fans anya wannan so ne? Wallahi duk matar da zatayiwa mijinta haka da sunan so ni nace ƙarya ne ba so ba ne, so yana nufin sadaukarwa da tana ƙaunarshi dole taso abin da ya ke so ko da zuciyarta ba ta so, mata mu kiyaye kanmu akan wannan haukan banzan da ya ke zamewa mace nadama daga ƙarshe.)

Buɗe idamuwanta tayi hawaye na ƙwarara, domin zuciyarta ta ƙeƙashe dole ta aikata mishi hakan, hannunta na rawa ta zame mishi wando, daidaitawa wuƙar da zatayi taji an riƙe mata hannu tare da ƙwasa mata wani gigitaccen marin da yayi sanadiyar ɗaukewar ganinta na wucin gadi.

Kafin ta dawo daga natsuwarta taji muryarshi cikin ƙaraji da kururuwa. "Tabbas ada na ɗauka ƙaunata ce yasa kike aikata dukan haukanki da baƙin kishinki, amma yanzu na fahimta so na ne bakiyi burinki ki ga nabar doran duniya, abin da baki sani ba Wasila, tun da naga kin yi wancan tunanin zuciyarki bata karaya ba yasa naji ajikina tabbas akwai wani tuggun da kika shirya, shine dalilin yin barcina na ƙarya domin na ga iya gudun ruwanki, Wasila na tsaneki bana ƙaunarki, ban taɓa tunanin zaki iya kashe ni ba, ada ina tausayinki bawai ban iya faɗa ba ne a a inayi ne saboda ƙauna da son zamanmu lafiya amma yanzu na fahimta ke ba irin mace da za'a zauna da ke ba ce, da safe ki bar min gida na sake ki saki ɗaya bisa adalci, bazan haɗaki da hukuma ba kin ci darajar yayanmu bazan so bar musu abin faɗa ba, amma ki sani ni Bashir na tsane ki."

Sosai Wasila ke kuka daga zaunen da ta ke, jin ya saketa yasa ta sakin wani gigitaccen kuka rarrafe ta fara cikin kukan nadama da danasani ta ke cewa "Bashir nayi kuskure, fon Allah kayi haƙuri ka ya femin" Bai kulata ba ya bar gurin.

Ranar Wasila batayi barci ba.

Wata biyu kenan da sakin har lokacin bata tafi gida ba, amma ko kallon ɗakinta Bashir ba ya yi, soyayya sabuwa kuwa tsakaninshi da Hafsat, Wasila ta zamo abin tausayi, tayi baƙi ta rame ta jeme ta kama yaranta ta damke tana basu kula, duk yarda taso da nunawa Bashir tayi nadama yaƙi fuskantarta, daga ƙarshe ganin ta kusa idda kar iddarta ta ƙare bai mayar da ita ba ta je gurin Hajiyarshi tana kuka akan tayafe mata ta tuba kuma ta roƙar mata Bashir ya fiya.

Sosai Hajiyar ta mata nasiha sannan ta kira Bashir ta basa haƙuri har lokacin

ba wanda yasan da sakin tsakaninsu.

Daman shima tuni a zuciyarshi ya mayar da Wasilar sai dai bai kulata ne sabod yana so ta gane kurenta, ai kuw ta gane domin ta koma ga Allah tana roƙon ya fiyarshi, daga ƙarshe Bashir ya ce ya mayar da ita kuma ya yafe mata.

Yanzu zamansu lafiya suke cike da son juna, yaranta tana basu kula, yanzu duk wacce taga tana haukan kishi ko ta ce tafi ƙarfin kishiya har gida ta ke zuwa ta mata nasiha sosai.

KARSHE.

KARSHE KENAN, DAN ALLAH A NUNA MIN KAUNA TA HANYAR YIWA LABARIN VOTING DA ZARAR AN TURO MANA LINK KUMA ZAKU GANSHI, INA MATUKAR KAUNARKU MUSAMMAN MUTANAN FACEBOOK NA GA KAUNA, JINJINAR BAN GIRMA GARE KU, BAZAN MANTA DA KUBA DA KAUNAR DA KUKA NUNA MIN DA LABARINA, JINJINA GA PRINCE ISMAIL AMINU FATAN ALKHAIRI BAZAN TAƁA MANTAWA BA DA KARAMCINKA BA ƊAN UWA ALLAH YA SAKA DA ALKHAIRI YA KAWO MATA TA GARI, SANNAN NURADDEEN SHUAIBU LIGHT INA GODIYA DA JINJINA.

To my fans a temaka amin share sannan ayi comments sabi da Allah da girmanshi, sannan kar a manta da vote□□Sharing sabi da girman Allah sannan a yi min voting sabi da girmanshi idan na turo link ɗin.□□😍